Lallai kowace Alumma tana da Amintaccen ta, kuma lallai amintaccen wannan Al-umma shi ne Abu Ubaidah Bn Al-Jarrah

An rawaito daga Anas Bn Malik -Allah ya yarda da shi daga Manzon Allah: "Lallai kowace Alumma tana da Amintaccen ta, kuma lallai amintaccen wannan Al-umma shi ne Abu Ubaidah Bn Al-Jarrah"

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

A cikin kowace Al-umma daga cikin Al-ummai wani Mutum da ya shahara da Amana sama da kowa, kuma mafi Shaharar wannan Al-ummar da Amana shi Abu Ubaidah Amir Bn Al-jarrah -Allah ya yarda da shi- saboda shi koda yake amanar ta kasance sifa ce da kowa daga cikin sahabbai yayi tarayya da shi a cikinta -Amincin Allah ya tabbata a gare su- sai sigar Hadisin tana nuna cewa ya xaresu a cikinta

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/11190